# SŨRATUL ‘AṢR سُورَةُ العَصۡرِ

Tana bayãnin cẽwa kõme mutum ya yi a lõkacinsa hasãra ne da ɓarnar zarafi, sai fa idan ibãda ce yake yi.

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Ina rantsuwa da zãmani.(1)

*2.* Lalle ne mutum yana a cikin hasara,

*3.* Fãce waɗanda suka yi ĩmani, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, kuma suka yi wa juna wasiyya da bin gaskiya, kuma suka yi wa juna wasiyya da yin haƙuri (su kam, ba su cikin hasara).

وَٱلۡعَصۡرِ ١
إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَفِي خُسۡرٍ ٢
إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡحَقِّ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ ٣

(1) Wasu suna fassarawa da waƙatin sallar Asar da kuma marece. A kõwane dai, an bai wa waƙati muhimmanci, zãmani yana yanke wanda bai yanke shi ba. Bã yã halatta ga mutum wata mudda ta zãmani ta wuce shi bai san amfãnin da ya sãma wa kansa a cikinta ba, kuma kõme ya sãmu idan ba addini ba ne, to, hasãra ce.